# Littafi mai Tsarki na yara

**Ke gabatar da**



# Sarki Dawuda (sashi na biyu)


**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Lazarus**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**



**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**




**Dawuda ne sarkin Yahuda, a kudancin Isra'ila. Amma sauran Isra'ila suka dauki Ishboshet, Dan Shawulu, a matsayin sarki. Yaki ya barke har shekaru bakwai. Amma Dawuda ya karu da karfi da girma.**



A karshe an kashe Sarki Ishboshet ta wurin sojojinsa biyu.



3

Sai duka dangogin Isra’ila suka zo wurin Dawuda suka shafe shi ya zama sarki a bisan Isra’ila. A karshe, Dawuda ya zama sarki a bisan duka al’umman Isra’ila.



4

Abu na farko wanda Sarki Dawuda ya yi shi ne ya kwace Urushalima. Sai ya zama birnin Dawuda. Ya sake gina shi da katanga mai karfi don abokan gaba. Daga Urushalima, sojojin Dawuda suka fita domin su yi nasara a kan Filistiyawa da sauran abokan gaban Isra’ila.



5



Biye da shi, Sarki Dawuda ya dawo da Akwatin Yarjejeniya na Allah zuwa Urushalima. Akwatin Yarjejniyar na Allah yana kunshe da Dokoki Goma da dokokin da Allah ya ba Musa. Wannan Akwatin yana tunashe Isra’ilawa tsarkin Allah da bukata su yi biyayya gareshi.

6



Dole Dawuda ya yi yake –yake dayawa a farkon kwanakin mulkinsa. Shi soja ne mai hikima kuma mutum ne mai tawaliyu wanda yake addu’a ga Allah domin bishewa.

7



Abin ya dame Dawuda da ganin cewa yana zama a gida mai kyau amma Akwatin Yarjejeniyar na Allah yana zama a tenti. Sai Dawuda ya dauki niyya zai gina haikali. Natan, annabin Allah, ya ce masa ya ci gaba.

8


A daren nan, Allah ya aika da sako zuwa wurin Dawuda: “Dan hidimana Dawuda, UBANGIJI zai yi maka gida. Sa’ad da kwanakinka suka cika ka kuma koma wurin hutu da kakaninka, zan shirya dan ka ya zama sarki bayan ka. Zai gina gida saboda sunana, kuma zan kafa kursiyin mulkinsa har abada.”
9


Dawuda ya so ya taimaki wadanda suka tsira daga iyalin Shawulu. Sai yaron Jonatan, mai suna Mefiboshet ne kadai ya samu, wanda shi gurgu ne. “Zai ci tare da ni a teburina kamar daya daga ‘ya’yan sarki.” Dawuda ya ce. Dawuda ya nuna wa Mefiboshet kirki saboda Jonatan babban amininsa ne.
10


Muddin Dawuda ya amince da Allah ya kuma yi biyayya gare Shi, Allah ya taimaki Dawuda ya yalwata. Amma wata rana, wani mummunan inuwa ya fadi a kan rayuwar Dawuda. Ya tura sojojinsa domin su yi yaki, sa’d da shi yana zaune a Urushalima. Wata rana da daddare, bai iya ya yi barci ba. Sai yana yawo a kan gidansa a sashin sama sai ya dubi birnin.
11


Sai ya ga wata mace kyakkyawa tana wanka. Sunan ta Betsheba. Dawuda ya yi zunubi da Betsheba ko da yake maigidanta, Uriya, daya ne daga sojojin Dawuda mai karfin hali. Sa’ad da Betsheba ta gaya wa Dawuda tana da juna biyu, sai Dawuda ya sani cewa zunubinsa yana kawo damuwa sosai.
12


Maimako ya tuba ga Allah, Dawuda ya yi kokarin rufe zunubinsa. Wannan bai yi ba! Ya kira Uriya ya dawo gida daga bakin daga, da nufi cewa Uriya zai ga kamar yaron da za a haifa nasa ne. Amma Uriya ba zai zauna a gida bayan yan’uwansa sojoji suna a bakin daga ba. Uriya ya kwana a bakin kofar gidan sarki.
13


Sai Dawuda ya kara aikata wani mummunan abu kuma. Sai ya komar da Uriya da mummunan wasika. Wasikar ta gaya wa shugaban sojojin ya tabbata Uriya ya mutu a wannan yakin. Bayan da aka kashe Uriya, sai Dawuda ya dauki matarsa ta zama nasa.
14

**Allah ya aiki bawansa Natan, domin ya nuna wa Dawuda zunubinsa. Natan ya gaya wa Dawuda labari game da wani mutum mai arziki da wani marar arziki. Mai arzikin yana da tumaki dari bisa dari. Marar arzikin kuma yana da guda daya ne kawai, 'yar karama, wadda yake rikewa kamar 'yarsa.**



15

**Sa'ad da wani mai tafiya ya zo gidan mai arzikin, sai mai arzikin bai kashe daya daga cikin tumakinsa don ya ciyar da bakon ba. Maimako, sai ya dan rago na talaka ne ya yanka wa bakon.**



16

**Dawuda ya yi fushi da sonkai na wannan mai arzikin. Ya yi kuka, "Mutumin da yi wannna lallai za a kashe shi."**



17

**"Kai ne wannan mutumin!" Natan mai karfin hali ya gaya wa Dawuda. Abin da Dawuda ya yi ya fi muni ga abin da mai arzikin ya yi a labarin.**



18

**Allah ya nuna wa Dawuda yadda abin da ya yi mugun abu ne. Dawuda ya tuba daga zunubinsa. Ya gaya wa Allah: "A gareka kadai na yi laifi na yi abin da ke mugu." Allah kuwa ya yafe zunubin Dawuda. Amma 'yar jaririn Betsheba ta yi rashin lafiya, sai ta mutu bayan haifuwa.**



19

**Allah ya yafe wa Dawuda muguwar zunubin nan. Sa'an nan Betsheba ta sake haifi wani yaro, Solomon, wanda ya zama babban sarki bayan Dawuda. Amma Sarki Dawuda ya kasance da 'ya'ya da yawa, wadansu daga cikinsu suka kawo masa bakin ciki.**



20

**Sarki Dawuda (sashi na biyu)**

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**2 Sama’ila 1-12**

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**






21

60



**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**